مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ﴿٢﴾

2. "Daga sharrin abin da Ya halitta.

وَمِن شَرِّ غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ ﴿٣﴾

3. "Da sharrin dare, idan ya yi duhu.

وَمِن شَرِّ ٱلنَّفَّٰثَٰتِ فِى ٱلْعُقَدِ ﴿٤﴾

4. "Da sharrin mãtã mãsu tõfi a cikin ƙulle-ƙulle.

وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ﴿٥﴾

5. "Da sharrin mai hãsada idan ya yi hãsada".

## SŨRATUN NÃS سُورَةُ النَّاسِ

Tana karantar da yadda ake nẽman tsari daga sharrin Shaiɗan na mutum da na aljani.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ﴿١﴾

1. Ka ce "Ina neman tsari ga Ubangijin mutane.

مَلِكِ ٱلنَّاسِ ﴿٢﴾

2. "Mamallakin mutane.

إِلَٰهِ ٱلنَّاسِ ﴿٣﴾

3. "Abin bautãwar mutane.

مِن شَرِّ ٱلْوَسْوَاسِ ٱلْخَنَّاسِ ﴿٤﴾

4. "Daga sharrin mai sanya wasuwãsi, mai ɓoyewa.[1]

ٱلَّذِى يُوَسْوِسُ فِى صُدُورِ ٱلنَّاسِ ﴿٥﴾

5. "Wanda ke sanya wasuwãsi a cikin ƙirãzan mutane.

مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ ﴿٦﴾

6. "Daga aljannu da mutane."

---

(1) Shaiɗan yakan ɓõye idan ya ji an ambaci sunan Allah, dõmin haka aka yi masa suna mai-ɓõyewa, wãto bã ya zamã wurin da ake karatu da wa'azi, kamar yadda bã ya zama cikin zũciyar mutum mai ibãda da gaskiya. Ibãda ta gaskiya ita ce wadda aka yi ta kamar yadda Allah Ya ce a yi ta. Banda ibãdar bidi'a, bã tã korar Shaiɗan. Kuma da sharaɗin a yi ibãdar da kyakkyawar niyya, dõmin aikin da bãbu niyya mai kyãwo game da shi ɓãtacce ne.